### Matsayin ingantaccen iri a shekara 2011

### daga Clive James, shugaban kungiyar ISAAA

*Sadaukarwa ga mutane miliyan dubu daya (1billion) dake fama da fatara da yunwa a fadin duniya*

---

## Yanzu haka filayen noman ingantaccen iri sai kara bunkasa a cikin shekaru goma sha biyar suke musamman a yanzu da yawan al'umma duniya yakai miliyan dubu bakwai

A dalilin moriyar da ake samu daga ingataccen irin shuka, an samu matukar bunkasar yawan wannan moriya a shekara ta 2011 da kimanin hekta miliyan goma sha biyu (12) inda a duk shekara ake samun bunkasa da kashi takwas cikin dari (8%) inda yanzu aka samu hekta miliyan dari da sittin (160,000,000) kari akan hekta miliyan dari da arba'in da takwas (148, 000,000) a shekara ta 2010.

Wannan kari da aka samu daga hekta miliyan daya da dubu dari bakwai (1,700,000) a shekara ta 1996 zuwa hekta miliyan dari da sittin (160miliyon) a shekara ta 2011 shi ya tabbatar da cewa ingataccen iri wata gagarumar nasara ce da aka samu a baya-bayan nan cikin sauri a tarihi.

Wani babban abin al'fahari a game da wannan inagataccen iri da aka bunkasa kwayar halittarsu daga shekara ta 1996 zuwa ta 2011 miliyoyin manoma ne a kasashe ashirin da tara (29) dake fadin duniya, da kashin kansu suka shuka da kuma kara shuka wadanna tsirrai sau miliyan dari (100'000'000) daya haifar da samun amfani daya kai na hekta miliyan duba daya da dubu ashirin da biyar (1.25 billion) hakan shi ya tabbatar da irin yadda yarda da amincewar da manoman suka yi da wannan fasaha- ta ingantaccen iri na samar da babbar moriya mai dorewa dake bunkasa tattalin arziki da muhalli.

Kasashe ashirin da tara ne (29) a shekara ta 2011 za su shuka wannan ingataccen iri goma sha tara (19) daga cikin kasashen, kasashe ne masu tasowa a yayin da sauran goman (10) kasashen, kasashe ne masu arzikin masana'antu wadannan kasashe goma (10) kowannensu na shuka abinda yafi hekta miliyan daya,(1 miliyon) kuma wadanda a nan gaba sune za su zama tubalin bunkasar wannan fasaha.

Haka kuma a shekara ta 2011 an samu yawan monoman da suka kai miliyan goma sha shida da dubu dari bakwai (16, 700'000) watau an sami Karin manoma miliyan daya da dubu dari uku (1,300,000) watau Karin kashi takwas cikin dari (8%) daga shekara ta 2010 sannan wadannan manoma kashi chasa'incikin dari (90%) ko kuma kimanin miliyan goma sha biyar (15 miliyon) masu karamin karfi ne daga kasashe masu tasowa, sannan a shekara ta 2011 a samu kananan manoma miliayan bakwai (7miliyon) daga kasar Sin da kuma Karin wasu kananan manoma miliyan bakwai (7 miliyon) daga kasar Indiya da suka zabi a wannan shekara su yi amfani da wannan fasaha ta inagataccen irin auduga da ya kai hekta miliyan goma sha hudu da dubu dari biyar(14, 500,000).

A shekara ta 2011 kasashe masu tasowa ne suka noma kashi hamsin (50%) na ingantaccen iri a yayinda a shekara ta 2012 kasashen ake hasashen za su zarta abinda kasashe masu arzikin masana'antu suka noma. Bunkasar wannan iri tana faruwa ne a cikin sauri ayayin da bunkasar zata lunka har sau biyu a kasashe masu tasowa daya kai har kashi goma sha daya cikin dari (11%) ko kuma hekta miliyan takwas da dubu dari biyu (8,200,000) wanda hakan ya dara kashi biyar cikin dari (5%) ko kuma hekta miliyan uku da dubu dari takwas (3,800,000) a kasashe masu arzikin masana'antu.

Iri daban-daban na wadananna ingantaccen iri nada matukar mahimmanci- ga misali kasashe goma sha biyu (12) suka shuka ingantaccen irin tayin amfani da a kalla kalar irin biyu (2) ko sama da haka a shekara ta 2011, abin sha'awa tara(9) daga cikin wadannan kasashe, kasashe ne masu tasowa ne wadannan da suka noma hekta miliyan arba'in da biyu da dubu dari biyu (42, 200,000) sama da kashi daya bisa uku na hekta miliyan dari da sittin (160 miliyon) da aka noma a shekara ta 2011, watau an samu Karin hekta miliyan talatin da biyu da dubu dari uku (32, 300,000) ko kuma kashi ashirinda biyu cikin dari (22%) na hekta miliyan miliyan dari da arba'in da takwas (148 miliyan) da aka noma a shekara ta 2010.

Kasashe masu bunkasa biyar (5) da suka fi noma ingantaccen iri sune Indiya da kasar Sin a nahiyar Asiya, sai Kasashen Birazil da Ajentina a Nahiyar Amurka ta kuda, da kuma kasar Afrika ta kudu a nahiyar Afrika, wadanda yawan al'ummar su ke matsayi kashi arba'in (40%) na yawan al'ummar duniya. Wadanda ake hasashe zasu haura mutum miliyan dubu goma (10 billion) nan da shekara ta 2100.

Kasar Birazil a shekaru uku (3) da suka gabata ita ce ke jagorantar bunkasar noman ingantaccen iri da ta zarce kowace kasa a fadin duniya inda ta bunkasa filin noman da hekta miliyan hudu da dubu dari tara (4,900,000) watau Karin kashi ashirin (20%) kenan cikin dari daga shekara ta 2010. An kara amincewa da wasu sababbin kalar irin da za'a yi amfani dasu a shekara ta 2011 wadananna iri sun hada da wani sabon iri na wake da aka bunkasa a cikin gida wanda yake bijirewa kwayar cutar virus wanda sashen hulda jama'a na EMBRAPA suka bunkasa (Ma'aikatar binciken da ta shafi aikin gona ta kasar Birazil).

Kasar Amurka tana cigaba da kasancewa jagora a matsayin kasar da tafi samar da ingataccen iri a fadin duniya da ke da filin noma da ya kai hekta miliyan sittin da tara (69 miliyon) wanda ake iya noma kashi chasa'in (90%) na kala-kalan irarawa na ingataccen iri, inda za'a cigaba da noma wani iri mai suna RR®alfalfa da yawansa yakai har hekta dubu dari biyu(200,000),

## Bayanai akan matsayin inagantaccen na sayarwa a fadin duniya na shekara ta 2011

Haka kuma an amince da wani sabon iri mai suna RR®sugarbeet wanda iri ne na papaya mai bijirewa kwayar cutar Virus da za’a noma hekta dubu dari hudu da dubu saba’in da biyar (400,75000) daga kasar Amurka wanda ya sami amnicewa a matasayi abinci a kasar Japan daga watan disambar shekara ta 2011.

Kwanan nan ne kasar Indiya tayi bikin cika shekara goma (10) na noma ingantaccen irin auduga inda a karon farko suka shukar data zarce hekta miliyan goma (10 miliyon) inda ya kai hekta miliyan goma da dubu dari takwas (10,800,000) watau kashi tamanin da takwas cikin dari (88%) na bunkasar yawan Auduga data kai hekta miliyan goma sha biyu da dubu dari biyu(12,200,000). Wadanda zasu ci wannan gajiya kananan manoma ne inda kowanen su a kalla yana noma audugar data kai hekta daya da rabi a kasar ta Indiya.kasar Indiya ta bunkasa kudaden shiga da ake samu daga sana'ar noma daga ingataccen irin auduga daya kai daga dalar Amurka miliyan dubu tara da dubu dari tara (9billion) a tsakankanin shekara ta 2002 zuwa 2010 ya zuwa dalar Amurka miliyan dubu biyu da dubu dari biyar (2.2billion) a shekara ta 2010 kachal.

A kasar Sin kuwa kananan manoma miliyan bakwai ne wadanda a kalla kowanensu ke noma rabin hekta suka sami nasarar noma yawan audugar data kai hekta miliyan uku da dubu dari tara (3,900,000) da kashi saba'in da daya (71%) . haka kuma samun yardar sayar da ingantaccen irin shikafar Golden wanda aka dade ana jira a kasar Filifins daga nan zuwa shekara ta 2013 zuwa ta 2014 zai tallafa sosai a kasar Sin.

kasar meziko ma na noma irin Audugar da aka inganta da yakai yawan hekta dubu dari da sittin da daya da dari biyar (161,500) da nasara ta kashi tamanin da bakwai cikin dari (87%) wanda hakan ya sa aka samu gagarumar nasara ta karin hekta dubu hamsin da takwas (58,0000) akan shekara ta 2010 watau kashi dari da saba'in da takwas (178%) ke nan. babban buri dai shine samar da isashshiyar auduga, sannan kuma a jihohin arewacin kasar ana noma ingantancen irin masara da aka bunkasa kwayar halittarta domin samar da masarar data dara tan goma (10) domin rage kashe kudin shigo da masara.

haka kuma nahiyar Afrika ma ta samu bunkasa a ta wannan fanni. domin kuwa kasashen Afrika ta kudu, Burkina faso da kuma Masar indan aka hada su sun noma abinda ya kai hekta miliyan biyu da dubu dari biyar (2,500,000), sannan kasashe uku na Najeriya Kenya da kuma Uganda sun gudanar da noma na gwaji mai yawa.

Bugu da kari kasashe turai guda shida sun sami nasarar shuka hekta dubu dari da goma sha hudu (114) na ingatanta irin masara watau an samu Karin kashi ashirin da shida ciki dari kenan (26%) daga shekara ta 2010 sanan an samu Karin kasashe biyu da shuka irin ingantacce na dankalin turawa mai suna “Amflora”.

Daga shekara ta 1996 zuwa 2010 wannan fasaha ta bunkasa kwayar halittar tsirrai ta taimaka wajenn samar da isashen abinci da kuma rage dumamar yanayi watau ta samar da Karin abinci da ya kai na dalar Amurka miliyan dubu saba’in da takwas da dari hudu (78.84 billion) da samar da kyakkyawan mahalli ta hanyar rage amfani da maganin kashe kwarin daya kai kilogram miliyan dari hudu da arba’in da uku (403 miliyon) a shekara ta 2010 kachakal watau an rage yawan fitar da iskar gas ta kabon di ozzaid da kilo miliyan dubu goma sha tara wanda dai dai yake da kauda motoci miliyan tara (9 miliyon) daga bin hanyoyi sannan kuma hakan ya ceci hekta miliyan chasa’in da daya (91miliyon) da kuma tallafawa yaki da talauci ga kananan manoma miliyan goma sha biyar (15 miliyon) wadanda ada suna daya daga cikin wadanda suka fi talauci a fadin duniya. Ingataccen irin shuka yana samar da isashen abinci sai dai ba zai iya zama kyakkyawar hanyar noma ba watau abin daya shafi jujjuya abinda ake nomawa shekara-shekara da kuma kaucewa bijirewar kwari da sauran cututtukan tsirrai, ingantaccen iri yafi dacewa da aikin noma gama gari ko kuma na yau da kullum.

Sai dai akwai bukatar dake da kwai cikin gaggawa a kirkiri wasu ka’idoji na kimiyya kayyadaddu a kasashe kanana da matalautan da kasashe da kuma kasashen turai game ingataccen iri.

Tantagaryar ingantaccen iri a shekara ta 2011 a fadin duniya ya kai na kimanin dalar Amurka miliyan dubu goma sha uku (13 billion) ana kuma samun amfanin kayan gona na sayarwa da suka kai dalar Amurka miliya dubu dari da sittin (160 billion) a shekara.

Akwai gwarin gwuiwa matuka akan amfanin da za’a samu nan gaba har ya zuwa shekara ta 2015 watau shekarar cimma muradun karni ta MDG da gaba da ita inda sabbin kasashe goma (10) zasu fara amfani da wannan fasaha, akwai shirin samar da ingantaccen irin masara da zai iya jurewa fari a nahiyar Amurka ta arewa nan da shekara ta 2013 da kuma a nahiyar Afrika a shekara ta 2017; sai kuma ingantaccen irin shinkafa ta Golden a kasar filifins a tsakanin shekara ta 2013 zuwa ta 2014; sannan sai kuma kasar Sin inda ake da kwarin gwuiwar samun karuwar yawan ingataccen irin masara da zai kai hekta miliyan talatin (30 miliyon) ko kuma sama da haka da kuma ingataccen irin shikafa. Ingantaccen iri tsirren da aka bunkasa kwayar halittar zasu tallafa gaya domin cikar burin cimma muradin karni nan da shekara ta 2015 na rage yawan fatara da talauci a fadin duniya ta hanyar kara samar da hanyar inganta samar da abinci, kuma ana iya kara bunkasa hakan ta hanyar hadingwuiwa tsakanin gwamnati da kuma yan’ kasuwa misali ingantaccen irin masara dake jurewa fari a nahiyar Afrika wanda gidauniyar nan ta Bill and Milinda Gates ta Attajirin nan dan kasar Amurka dake bada tallafin jin kai ke taimakawa.

ISAAA’s sun mayar da hankalisa ne kan musayar bayanai na sabbin fasaha da kuma samun hanyoyin hada hannu da wannan gidauniya ta Gates musamman kan wata bukata da suka mikawa kasashen nan masu karfin tattalin arziki na G20 a watan Nuwambar shekara ta 2011.

An samar da cikakke bayanai a ISAAA’s na bayani Arba’in da uku (43) na Ingantaccen iri na sayarwa a fadin duniya na shekara ta 2011”, wanda Clive James ya rubuta. Domin samun cikakken bayani sai a ziyarci sashen yanar Gizo http://www.isaaa.org or contact ISAAA AfriCenter at +245 20 4223618, or email to africenter@isaaa.org or info@isaaa.org